# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tsabta
## Kashi na huɗu: Neman Sama'ila

Wanda ya rubuta: Nkoji C. Muhoho
Wanda ya tace: Maja Braun
Wanda ya fassara: Kabir Isa Jikamshi

**'Yan wasa:**

| | |
|---|---|
| Sama'ila: | ɗan shekara 17 |
| Bilkisu: | 'yar shekara 40 |
| Mariya: | 'yar shekara 43 |
| Adamu: | ɗan shekara 36 |
| Dokta Husaina: | 'yar shekara 34 |

**MAI GABATARWA:**

Jama'a, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu" a kan kiwon lafiya inda ake magana a kan yadda za a nisanci kamuwa da cutar gudawa. A wasan da ya gabata kun ji cewa, jinjira Fati ta rasa ranta a sanadiyyar cutar gudawa, yayin da kuma wanta, Sama'ila, shi ma yake fama da rashin lafiya a gida. Har yanzu wannan iyali yana cikin jimami dangane da wannan baƙin labari game da rasuwar wannan jinjira. Amma kuma sun baro asibitin da aka kwantar da wannan yarinya a cikin hanzari, saboda su koma domin kulawa da Sama'ila da ke fama da jinya. Dole ne a samu hanyar kuɓutar da ran Samaila daga cutar gudawa da sakamakon da takan haifar.

**Fitowa ta 1: A gidan Bilkisu**

Mariya, Hadiza, Bilkisu, Dokta Husaina

| | |
|---|---|
| **MARIYA** | Bilkisu da kuma ke 'yata Hadiza! Wai me ya sa kuka daɗe haka? Na maƙale a nan wurin Sama'ila. |
| **HADIZA** | Sama'ila, Sama'ila! |
| **MARIYA** | Hadiza. Mene ne yake damun wannan yarinya ne? Sai kai kuma Adamu da matarka Likita Husaina. Mene ne ya sa na ga dukan fuskokinku babu wani annuri? |
| **HADIZA** | Sama'ila, Sama'ila! Ina! Sama'ila zai mutu. Kada ka mutu, Sama'ila! Wayyo! |
| **MARIYA** | Tsaya! Dakata a nan, Hadiza, dakata! Ina dabarun naki suke? Ki daina ingiza mutane a kan hanyoyinki! Kuma shin wai ma ina za ki ne? |
| **BILKISU** | Wayyo Allah, wayyo Allahna! Yanzu kam kowa ya mutu. Cutar gudawa, ni ma sai ki zo ki tafi da ni! |

| | |
|---|---|
| **MARIYA** | Bilkisu**,** shin ko wani zai iya faɗa mini abin da yake wakana? Kuma ina jinjira Fati? Tana barci a cikin mota ne? Kun fa san cewa, kusan ko da yaushe a cikin kuka da barci take. |
| **DR HUSAINA** | Mariya, jinjira Fati ta rasu! |
| **MARIYA** | Me? Me kika ce, Dokta Husaina? Ina! Ba zai yiwu ba. Wayyo, ƙawata Bilkisu, ki gafarce ni. Ban sani ba. Ya kamata ki faɗa mini nan take. Wayyo! A'a! Don a ce na gasa ayabar nan tun tuni, mai yiwuwa da ta taimaka. Yanzu, ga shi jinjira Fati ta... |
| **DR HUSAINA** | Kada ki ɗaura wa kanki laifi, Mariya. Babu wata hanya da wannan ayabar za ta iya taimakawa. |
| **BILKISU** | Yanzu mene ne abin yi? |

**MAI BA DA LABARI:**

A daidai wannan lokaci da kowa yake juyayin Fati, abin tausayi, Hadiza tana can ta samu isa ɗakin Sama'ila inda ta same shi duk ya tsotse. Hasali ma ba ta sani ba, ko ma yana da rai?

**Fitowa ta 2: A ɗakin Sama'ila**

Hadiza, Sama'ila, Dokta Husaina, Mariya

| | |
|---|---|
| **HADIZA** | Sama'ila, Sama'ila! Ko ka mutu ne? Ka mutu ne? |
| **SAMA'ILA** | E, Hadiza, na tashi daga aiki. Yadda nake ji, ni ma zan iya mutuwa… |
| **HADIZA** | Don Allah, kada ka mutu, Sama'ila, kar ka mutu! Tashi, tashi! Ya kamata mu tafi asibiti. Idan kuma ba haka ba, cutar gudawa za ta kashe ka, kamar yadda ta yi wa jinjira Fati. |
| **SAMA'ILA** | Mene ne? 'Yar'uwata ta rasu? Wayyo Allahna! |

| | |
|---|---|
| **DR HUSAINA** | Sama'ila! Ka farka? Tashi! Na zo in tafi da kai asibiti. Assha, wannan ɗakin wari yake yi. |
| **SAMA'ILA** | Wai haka ne, labarin da na ji game da Fati, Anti Husaina? |
| **DR HUSAINA** | E, Sama'ila, ka yi haƙuri. Amma kuma abin da ya fi muhimmanci a halin yanzu, shi ne a kai ka asibiti yanzu! |
| **HADIZA** | Yana ƙoƙarin tashi. Ba zai iya ba. Jikinsa ya mutu liƙis. Ba zai iya tafiya da ƙafafunsa ba. |
| **SAMAILA** | Wayyo Allah! Na kasa yarda da batun da na ji game da Fati. Dokta Husaina, ni ma zan mutu? Ina fama da cutar gudawa, ko ba haka ba? Kuma mai yiwuwa ni ma ta zama ajalina. Ko ba haka ba? |
| **DR HUSAINA** | Idan har ba ka samu kulawar asibiti ba cikin gaggawa, kana fuskantar yiwuwar mutuwa. Tun yaushe ne ka fara rashin lafiya? Yaushe ka fara fahimtar cewa kana zuwa banɗaki a kai-a kai? |
| **SAMA'ILA** | Ban sani ba, Likita. Ina jin kusan… tun makwanni biyu da suka gabata. |
| **DR HUSAINA** | Lokacin ya yi tsawo da yawa! Kamata ya yi tun tuni ka je asibiti. Yanzu zo nan, bari in taimake ka. Cutar gudawa tana da hatsari sosai, musamman idan gudawar ya ƙi tsayawa. Dole mutane su riƙa tafiya asibiti ba tare da jinkiri ba. |
| **HADIZA** | Sama'ila, ba ka wanke hannunka ba. Shi ne dalilin da ya sa kake rashin lafiya. Na taɓa rera maka waƙata game da muhimmancin wanke hannu. Dole in koya maka wannan waƙa. |
| **DR HUSAINA** | Ba yanzu ba. Hadiza, bari mu taimaka masa, ya sanya kayansa. Daga nan mu kama hanyar zuwa asibiti. |
| **MARIYA** | M'm'm'm'm. Wannan wuri yana wari kamar wani lambatu ko masai. |

**DR HUSAINA** Yauwa Mariya, na yi murna ganinki a wannan wurin. Taimaka mini, mu shirya Sama'ila. Jikinsa ya mutu sosai, ba zai iya tafiya ba, ballantana ya iya sanya kayansa da kansa.

**MARIYA** Ke, kin ga. Kada ki buƙace ni da in taɓa wannan yaron! A duk tsawon ranar nan da kuka bar ni da shi na rasa inda zan sa kaina yana ta gudawa mai ɗan karen warin tsiya. Duk ya ɓata ko'ina. Duba wannan tufafin. Kalli don Allah!

**DR HUSAINA** Dakata, dakata! Mariya, kada ki taɓa kayayyakinsa da suka gurɓace ba tare da kin wanke hannuwanki ba don kariya. Yanzu, fita waje, fita da sauri! Mariya, tafi ki wanke hannuwanki nan take.

**MARIYA** Mene ne ya samu hannuwana? Na yi jinyar wasu mutanen marasa lafiya masu yawa. Babu wani bambanci da wannan.

**HADIZA** Malama ta ce, dole mu riƙa wanke hannuwanmu a ko da yaushe.

**MARIYA** 'Yammata, na sha faɗa miki cewa ke ba…

**DR HUSAINA** Mariya, ni ce likita a nan, kuma na umarce ki, ki je ki wanke hannuwanki sosai, yanzu-yanzu. Idan kuma ba haka ba, ke ce za ki kasance mutum na gaba wanda… Ta yaya kika bayyana lamarin ma? "Ban san kowane ɓangare ne zai iya gurɓata nan gaba ba." A taƙaice, muddin ba ki hanzarta wanke hannuwanki ba, cikin wasu 'yan sa'oi, ke ma za ki fara sakin gudawa ba ƙaƙƙautawa. Mariya, ki tafi yanzu-yanzu ki wanke hannuwanki.

**HADIZA** *Ku wanke hannuwanku,*
*ku wanke hannuwanku,*
*ku wanke hannuwanku*
*a yayin cin abinci.*
*Malallatan mutane*
*ba sa wanke hannu*
*a yayin cin abinci,*

*da zarar sun fito*
*daga banɗaki a kullum.*

**MAI BA DA LABARI:**
A daidai lokacin da suke taimaka wa Sama'ila ya tashi daga kan gado domin tafi da shi asibiti, ita kuwa Hadiza sai ta ci gaba da rera waƙa inda take sake tunatar da kanta da kuma duk wanda zai saurara cewa wanke hannuwa shi ne kaɗai zai iya nisantar da mutum daga kamuwa da cutar gudawa. Abin takaici, an yi rashin Fati. Amma ga alama ba za a yi asarar Sama'ila ba, muddin dai aka kai shi asibiti cikin hanzari.

**Fitowa ta 3: A asibiti**
Hadiza, Sama'ila, Dokta Husaina

| | |
|---|---|
| **HADIZA** | Sama'ila, suna yi maka ƙarin ruwa kamar yadda suka yi wa jinjira Fati…. Amma hakan bai taimaka mata ba. |
| **SAMA'ILA** | Dokta Husaina, na gode da kika kawo ni asibiti, amma a gaskiya na tsorata sosai. Na firgita, ina zaton ni ma zan mutu kamar ƙanwata Fati. |
| **HADIZA** | Sama'ila! Idan ka mutu Sama'ila, zan mutu. |
| **DR HUSAINA** | Shhh, babu wanda zai mutu. A gaskiya, bai kamata ma a ce, cutar gudawa ta zama ajalin mutane ba. Saboda da ni da ku za mu iya yin rigakafin kamuwa. Idan kuma aka kamu da ita, amma aka hanzarta yin maganinta, za a samu lafiya. Wannan abu ne mai sauƙi. |
| **HADIZA** | Na sani, Anti Husaina, na sani… |
| **DR HUSAINA** | Dole ku shaida wa iyayenku da abokai da sauran jama'a cewa matakan nisantar kamuwa da cutar gudawa suna da sauƙi ƙwarai. Haka nan ma, na magance ta. Kun gane? |

**SAMA'ILA** Kwarai da gaske.

**HADIZA** E, mun gane.

**SAMAILA** Mene ne suke yi da dukan samfurin da suka ɗauka daga wurina?

**HADIZA** Sai aka umarce ka, ka sanya bayan-gidanka da fitsarinka a cikin wata ƙaramar kwalba! Ha ha ha!

**SAMAILA** Anti Husaina kin ga, don Allah ki ce ta bari!

**DR HUSAINA** Zo nan Hadiza, ki ƙyale saurayinki ya sarara.

**SAMA'ILA** Ni ba budurwata ba ce!

**HADIZA** Ni ma ba saurayina ba ne!

**DR HUSAINA** Na yi murna ta cikin barkwanci, mun samu wannan bayanin mai muhimmanci. Yanzu kuma ai sai mu koma ga batun rashin lafiyarka ko, Sama'ila? Ka gani Sama'ila, na duba samfurin bayan-gidanka.

**HADIZA** Mhmmm!

**DR HUSAINA** Bayan-gida ruwa-ruwa ne, kuma akwai jini-jini da majina a cikinsa. Waɗannan alamomi ne na samun ƙwayoyin cutar *amoeba* a cikin jikin mutum, wadda da akan ɗauka a cikin ruwa, doron-ƙasa, cikin iska, da kuma cikin jinin mutum, waɗanda a dunƙule muke kira *amoebiasis*.

**HADIZA** Mhmmm!

**DR HUSAINA** Mai yiwuwa malaman kiwon lafiya a nan za su gano cewa mutum ya kamu da nau'in ƙwayar cuta mafi ƙanƙanta da ake kira *protozoa* mai kama da ƙwayar cutar cikin jini ta *amoebiasis*, wadda takan mamaye tare da cinye cikin 'yan hanjin mutum. Wannan shi ne yake haddasa jini-jini da majina a cikin bayan-gidan mutum mai yin zawo da muke kira cutar atuni.

**HADIZA** Wari!… Cutar atuni tana da wari.

**DR HUSAINA** E, Hadiza, ke ma za ki ji kamar kina wari!

**SAMA'ILA** Wannan shi ne abin da ya kashe ƙanwata Fati?

**DR HUSAINA** Babu bambanci a tsakaninsa da na ƙwayoyin cutar gudawa. Na yi amana cewa, wannan jinjira Fati ta yi fama ne da ƙwayar cutar *enteropathogenic* wadda take cutar da 'yan hanjin ɗan Adam.

**SAMA'ILA** *Entertho*–me?

**DR HUSAINA** Na yi murna, ka fara wartsakewa, har kana irin abin dariyar da ka saba yi! Shakka babu, ƙarin ruwa da abincin da ake ɗura maka suna aiki. Bari in yi ƙoƙarin yin bayani cikin kalmomi masu sauƙi. Abin da jinjira Fati ta yi fama da shi, irin naka ne, sai dai akwai ɗan bambanci. Wato ƙwayar cutar da ke cikin gubar da take fitarwa, wadda take cinye cikin 'yan hanji, suna samun saɓani da azamar gangar–jiki, ta iya ɗaukar ruwa da abinci mai gina jiki, waɗanda muke samu daga abin da muke ci da sha.

**HADIZA** Fati, abin tausayi.

**DR HUSAINA** O, ki gafarce ni, Hadiza. Ya kamata mu ƙyale Sama'ila shi kaɗai. Yana buƙatar samun hutu sosai, kafin ya iya warwarewa.

**HADIZA** Ina son zama a wurin Sama'ila. Zan iya zama a nan? Ina son kula da Sama'ila. Na yi alƙawari zan kula da shi sosai.

**DR HUSAINA** Hadiza, babbar kulawa da za ki bai wa Sama'ila a halin yanzu ita ce, ki ƙyale shi ya huta, ya maido da kuzarin jikinsa. Za mu sake dawowa gobe, domin mu duba shi.

**HADIZA** Kin yi mini alƙawari?

**DR HUSAINA** Ba shakka, Hadiza. Na yi miki alƙawari.

**MAI GABATARWA:**

Kun ji fa, masu saurarenmu, babban abin farin ciki shi ne, yanzu kam Sama'ila yana ci gaba da murmurewa. Ma'aikatan asibiti za su tabbatar da cewa ya warke garau ta hanyar ba shi magungunan da za su yaƙi ƙwayoyin cutar da suka haddasa masa yin fama da cutar gudawa. Ana iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe, idan ana muradin sake sauraro ko kuma aiko da tsokaci